


Ruhunsa Mai Tsarki a Cikin Mu



Ibada - Abincin Yini (Rana 47)
Daga Derek Prince

> Gama idan kuna rayuwa bisa ga ɗabi'ar jiki za ku mutu; amma idan bisa ga Ruhu kuke matasda ayyukan jiki, za ku rayu. (Romawa 8:13)

Bulus ya faɗa wa "Masu Bi na ruhu" cewa idan muna yin rayuwa bisa ga ɗabi'ar jiki, za mu mutu, domin muna kiwon abin da ke ruɓa. Ba abin da za ka samu sai ruɓa idan ka yi rayuwa bisa ga ɗabi'ar jiki.

Akwai gaba tsakanin jiki da Ruhu; babu jituwa tsakanin su. Shirin Allah na ceto shi ne ya kaswa da tsohon halin mutuntaka kuma ya samar da sabon hali gaba ɗaya ta wurin Ruhunsa Mai Tsarki a cikinmu. Ko da yake Allah ya yi tanadi gaba ɗaya domin wannan canji, dole ne mu aikata shi a rayuwarmu. Dole mu kashe ayyukan jiki. Allah ba zai yi mana wannan ba; Ya ba mu dama, iko, da ƙarfi, amma dole ne mu yi amfani da su.

Littafi Mai Tsarki ya ce:

> "Amma duk waɗanda suka karɓe Shi [Yesu], ya ba su iko su zama 'ya'yan Allah" (Yohanna 1:12)

Muna samun ikon lokacin da aka sake haifuwar mu. Amma ikon ba shi da amfani sai dai idan an yi amfani da shi. Sake haifuwa zarafi ne—dama ce da muka samu don zama wani abu mai ban mamaki idan za mu yi amfani da ikon da mu ke da shi. Idan ba ma ɗaukar matakai don yin amfani da ikon bisa ga maganar Allah a kan matsaloli da zunubai da ke fuskantar mu da manne mana ba, ba za mu ci gaba ba ko kaɗan.

Dole ne mu guje daga wani tunani—a cikin jiki—zuwa wani daban gaba ɗaya. Muna bukatar taimakon Ruhu Mai Tsarki.

> "Domin iyakar waɗanda Ruhun Allah ke bishe su, waɗannan [kuma waɗannan kaɗai] ne 'ya'yan Allah" (Rumawa 8:14)

Ibada - Abincin Yini

Kwafi: WD-B097-047-HAU
Sabunta ta karshe: 16 Feb 2026
Yanar Gizo: derekprince.com/ha/resources

